# MU SAN KAMANNIN ANNABI

## ƊABI'UNSA DA HALAYENSA DOMIN KOYI DA SHI

صَلَّى اللهُ عَلَيْهِ وَسَلَّمَ

DR YAHAYA TANKO

# MU SAN

# KAMANNIN ANNABI

# ƊABI'UNSA DA

# HALAYENSA

# DOMIN KOYI DA SHI

**(SALLALLAHU ALAIHI WASALLAM)**

**DR YAHAYA TANKO**

Ana son duk wanda yake son ya buga wannan littafi

ya nemi izini daga mawallafin.

An fara bugawa a shekaraR 1441 AH =2020M

ISBN:978-978-983-934-6

Maxaba’ar MJB printers Kano ta buga baljamo@yahoo.com

08069776038

**ABUBUWAN DA KE CHIKI**


| | |
|---|---|
| **Gabatarwa.** | **iii** |
| **KASHI NA FARKO** | 1 |
| KAMANNIN ANNABI KYAN HALITTARSA DA SUFFARSA. | 1 |
| MUHIMMANCIN SANIN ANNABI: | 1 |
| SUFFAR JIKIN ANNABI | 5 |
| **KASHI NA BIYU** | 11 |
| ƊABI’UN ANNABI DA HALAYENSA. | 11 |
| ƊABI’UN ANNABI | 11 |
| HALAYEN ANNABI | 18 |
| **KASHI NA UKU** | 36 |
| KO YI DA ANNABI | 36 |
| WAJIBCIN KOYI DA ANNABI | 36 |
| KOYI DA ANNABI A TSARIN RAYUWA | 40 |
| YADDA SAHABBAI SUKA YI KOYI | 45 |
| KAMMALAWA | 51 |

# GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah. Muna godiya gare shi, muna neman taimakonsa, muna neman gafararsa. Muna neman tsarin sa daga sharrin kawunanmu, da munanan ayyukanmu. Wanda Allah, shi kaɗai. Na kuma shaida Annabi muhammadu bawansa ne, kuma manzonsa ne. Tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.

Bayan haka, tunanin rubutu wanna ɗan littafi ya samu ne a cikin watan Sha'aban na shekarar hijira ta 1441, wanda yayi daidai da watan afrilu na shekarar miladiyya ta 2020.

Yadda abin ya faru shi ne, sauka muka yi a masallaci Umar Bin Kattab, ta wani littafi mai suna Ar Rahiƙul Mukhttab, wanda ya Ƙunshi Tarihin rayuwar Manzon Allah ( Sallallahu Alaihi Wasallam) To a ƙarshen littafin mawallafin ya cikasa shi da bayanin kamannin Annabi na halittar jikinsa da ɗabi'unsa da halayensa, ya sanya ɗaya daga cikin masu sadaukar da dukiyarsu wajen yin hidima ga wannan masallaci, ana kammalawa sai ya taso yazo inda nake, ya roƙi na fassara 'yan warƙoƙin da suke bayanin kamanin Annabi da halayensa, (waɗanda basu wuce shafi bakwai ba). Ya ce shi zai ɗauki nauyi bugawa.

To ni kuma matsalata gameda rubutu itace, ban cika sha'awar fassara kawai ba. Don haka sai rubuta wannan ɗan littafi. Na ɗebo abinda yake cikin wancen littafi da muka sauke, na ƙara da wasu bayanai waɗanda nake ganin suna da muhimmaci, na sawa littafin suna: MU SAN KAMANNIN ANNABI MUHAMMAD S.A.W DOMIN KOYI DA SHI.

Littafi ya ƙunshi fasalai uku (watau kasha-kashe guda uku): Kashi na farko na ba shi suna: KAMANNIN ANNABI, KYAN HALITTARSA DA SUFFARSA. Kashi na biyu na bashi suna: ƊABI'UN ANNABI S.A.W DA HALAYENSA. Shi kuma kasha na uku sai nab a shi suna: KOYI DA ANNABI MUHAMMAD S.A.W.

Muna rƙon Allah (SWT), shi wannan bawan Allah, Allah ya saka masa da alkhairi. Allah ya isar masa da niyyarsa ta buga wannan. Allah ya amfani jama'ar Musulmi da shi baki ɗaya, amin.

DR Yahaya Tanko.

08060846703

**KASHI NA FARKO KAMANNIN ANNABI MUHAMMAD (S.A.W), KYAN HALITTARSA DA SUFFARSA**

**Muhimmacin Sanin Kamannin Annabi:**

Abu ne mai matuqar muhimmaci ga musulmi ya san kamannin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) da suffarsa. Domin abinda mutum yake so ya kamata ya san shi. Kuma ma ai mukance: "Allah ya sa mu ga Annabi" watau a lahira. Kai ba ma sai a lahira ba. Babu shakka ganin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) a mafarki abu ne mai yiwuwa. Amma yaya za'a yi mutum ya san shi ya gani. Babu shakka sai mutum ya san kamanninsa sannan zai san, shi din ya gani a mafarki. Ga dai yadda lamarin yake a hadisin Abu Huraira (R.A):

"Daga Abu Huraira (R.A) ya ce: "Na ji Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana cewa: "Wanda duk ya gan ni a mafarki, to zai ganni a far ke. Shaiɗan baya kamantuwa da ni", (Bukhari da Muslim suka ruwaito). Imamul Bukhari y ace: Malam Ibnu sirina[1] ya ƙara da bayanin cewa: "Idan ya gan shi a kamanninsa". Ka ga ke nan dole sai mutum ya san kamanninsa. Idan

[1]Shi ne Muhammadu bin Sirina. Babban tabi'i, mutumin Basara. Malamin Tafsiri da Hadisi da Fiƙhu, Ya rasu a shekarar hijra ta: 110 yana da shekaru sama da tamanin, bayan rasuwar Hasnul Basari da kwana ɗari.

ba haka ba sai Sahaiɗan ya zo wa mutum a kamar da ba ta Annabi ba.

A wata ruwayar ta muslim: "Wanda ya gan ni a mafarki to zai gan ni a farke, ko kamar ya gan ni ne a farke. Shaiɗan ba ya kamantuwa da ni".

Wannan ya nuna cewa, lallai ne duk Musulmi ya san kamannin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam). Malamai sun yi ƙarin bayani gameda jimlar: (To da sannu zai gan ni a farke), inda suka ce, wannan jimilar ta zo a ɗayan ruwayoyin Muslim tare da nuna shakka daga mai ruwaya kan dayan biyu: Watau da ƙari kamar haka: "Ko kamar ya gan ni a faɗake".

Haka kuma ya zo a wata ruwaya kamar haka (haƙiƙa ya gan ni a farke)[2]. Watau, "Ni ya gani, gani na haƙiƙa"[3]

Abin nufi a nan shi ne, kada ka wahalar da kanka da fassarar masu cewa idan mutun ya gan shi a mafarki to zai gan shi a duniya, kuma a farke. Wannan ɓatacciyar fassara ce. Bata da tushe a addini. Abinda za ka fahimta shi ne, sauran ruwayoyin biyu qarfafa ganin suka yi. Wannan ya sa

malamai suka ɗauka ta farkon ma haka take nufi watau ƙarfafa ganin take nufi. Ba wai tana nufin za'a gan shi a farke a wannan duniyar tamu ba.

**Suffar Jikin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam):**

Allah (Subbahanahu wata'ala) ya fifita Manzonsa da kyan halitta, fiye da sauran bayinsa. Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) mutum ne madaidaicin halitta. Ba dogo ba, ba kuma gajere ba. Watau shi matsakaici ne.

Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) fari ne mai surkawa da jaja-jaja. Watau ba fari gau ba. Allah ya halicce shi da fuska mai haske. Yadda fuskarsa take a tsakanin mutane, kai ka ce farin wata ne, irin yadda yake haskaka sauran halittu  na duniya. Yana da yalwar goshi da karan hanci. Yana da gashin ido da na gira, masu duhu. Yana da tsagar baki mai ɗan tsayi, ba tsukakkiya ba. Haka nan yankan tsagar idanunsa su ma suna da ɗan tsayi. Ƙwayar idanunsa fara ce tas, baƙin kuma baƙi suɗuk. Wuyansa yana da ɗan tsayi. Yana da wushirya a tsakanin haqoransa na gaba. Gashin kan Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) baƙi ne wuluk, kuma mai tsayi. Wani lokacin, Idan ya bar shi, yakan kai iya kunnuwansa, daga bayansa. Kuma yakan zuba a kan kafaɗunsa. Yana da gemanya mai duhu. Kuma yana barinta ta yi tsayi. A ƙarshen rayuwarsa ya yi furfura a kansa da gemanyarsa, wadda bata fi qidaya ba.

Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana da faɗin ƙirji. Watau akwai faɗi a tsakanin kafaɗunsa. Cikinsa bas hi da tudu. Yana da gaɓoɓi watau ƙasusuwansa suna da girma. Akwai gashi daga tsakiyar ƙirjinsa zuwa cibiyarsa. Akwai hatimin annabta a gefan kafaɗarsa ta hagu, daga baya. Yana da tsayin hannaye madaidaita. Tafukan hannayensa suna da ɗan tudu da taushi. Ba a ƙarmashe suka ba. Haka nan kasangalalinsa da tafukan ƙafafuwansa. Amma ba shi da nama a agrarsa. Watau agurarsa a motes take. Tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi.

Daga is'haƙa ya ce:, na ji Barra'u yana cewa: "Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance ya fi kowa kyan halitta. Ba kuma gajere ba". (muslim ne ya rawaito)

Daga Aliyyu bin Abi Ɗalibin (R.A), ya ce: "Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) fari ne, mai cizawa da jaja-jaja" (Albani ne ya ruwaito a cikin aljami'us sahihu).

Daga Abdur Rahman ɗan Abdullahi ɗan ka'bu (yace. "Abdullahi ɗan ka'bu ya ce: "Na ji ka'bu ɗan maliku yana bayani game da (abin da ya faru sanda Allah ya karɓi tubansu na rashin zuwa masallaci), ya ce: Na yi sallama ga manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) alhali fuskarsa tana ƙyalƙyali saboda farin ciki ya kasance idan ya yi farinciki sai fuskarsa ta yi haske, kai ka ce wani yanki ne na farin wata. Mun kasance muna gane haka game das hi "(Bukhari ne ya ruwaito).

Galibi ana suffata fuskar Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) da farin wata, saboda haske da walwala da fuskarsa takan yi (musamman) a yayin da yake cikin farinn ciki. Wannan

yana nufin cewa, kamar yadda farin wata yake a duniya, to haka Annabi yake a cikin mutane. Amma a wannan Hadisin na Ka'abu bin Malik ya ware wani kashi ne na wata, domin yin ishara da goshin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam), inda hasken ya fi bayyana, a sanda yake cikin farin ciki. Shi ya sa ya keɓance shi da wani yanki na wata[4].

----------------------------

Duba Fathul Bari 122\8

Daga Abu Is'hak ya ce: An tambayi Barra'u (R.A), shin fuskar Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) kamar (hasken) takobi take? Sai y ace: "A'a", kamar (hasken) wata take" (Bukhari ne ya ruwaito)

Daga Jabir ɗan Samuratu, yace: "Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance mai faɗin baki, mai tsayin yankan idanu, Mai siraren maƙyangyama…" (Muslim ne ya ruwaito).

KASHI NA BIYU

**Ɗabi'un Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam)**

**Da Halayensa**

**Ɗabi'un Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam):**

Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance mai yawan murmushi da sakin fuska. Wani lokaci yakan yi dariya, har haqoransa na gaba ko wushiryasa ta bayyana. Idan ya yi fushi jijiyar fuskarsa takan kumbura da jini. Amma fa baya yin fushi domin an cuce shi, sai domin an saɓa wa Allah. Ya kasance mai nutsuwa da yawan zurfafa tunani. Ba shi da yawan wasa da kakaci koda dai yakan yi barkwanci (ko abin da ake kira zolaya), a wasu lokutan. Idan zai yi Magana yakan yi ta filla-filla, yadda kowa zai gane abin da yake nufi. Kalmominsa 'yan kaɗan sukan ƙunshi bayani masu yawa. Wannan shi ake kira (kalmomi 'yan kaɗan, waɗanda suka ƙunshi abubuwa masu yawa). Ya kasance yana da son ƙamshi, ba ya son wari ko kaɗan. Yana da son yin abubuwa da dama. Kamar taje kai da sanya takallmi da yayin yin wanka da dukkanin al'amuransa[5]. Yakan yi tafiya da takalmi, wani lokaci ba sai da takalmi ba. Yana yin tafiya cikin sauri, tare da ɗaga kan tudu. Idan zai yi waiwaye yakan juya da jikinnsa gabaɗaya.

Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance yakan yi zaman haɗe jiki. Watau yakan zauna cinyarsa a haɗe da cikinsa, alhali ya sa hannayensa ya haɗo qafafuwansa. A wasu lokutan akan ga ya yi rigingine, ya ɗora ƙafarsa ɗaya a kan ɗaya. Ya kasance idan zai ci abinci yakan ci a durqushe. Yana ci da 'yan yatsu uku. Musamman abincin da zai ciwu a haka. Kamar dabino da gurasa da sauransu. Idan zai sha ruwa ba ya yin numfashi a cikin mazubin, kuma yana sha a zaune. Kodayake a wasu lokuta a kan ga sha ruwa a tsaye. Ya zo a cikin As Shama'lun Nabawiyya cewa, Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana da son koren abu. Kuma ya fi son na ƙafafuwan ƙaramar dabba. Bai taɓa yin kwana uku yana ƙoshi da gurasar alkama ba. Ya fi cin gurasar sha'ir. Mu sani cewa shi sha'ir kamar alkama ya ke. Bai taɓa cin gurasar da romo ba har ya bar duniya. Watau sai dai da mai. Idan ya isa gidan mutane yakan tsaya a gefen dama na ƙorar gidan, ya yi sallama. Ya kasance idan zai kwanta yakan ɗora kansa a kan hannunnsa na dama, ya ambaci Allah, sannan ya yi bacci.

Daga ka'abun bin Malik (R.A) ya ce: "Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance fuskarsa takan zama kamar wani yanki ne na farin wata, idan yana farin ciki" (Bukhari ne ya ruwaito).

"Daga Aliyyu (R.A) ya ce: "Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance idan yana tafiya, yakan yi ta cikin sauri da ɗaga ƙafa, kamar yana gangarowa daga tudu", (Tirmizi ne ya ruwaito).

Amma idan yana yin tafiya tare da sahabbansa yakan sa su a gaba. Yakan ce: "Ku bar bayana domin mala'iku".

Idan Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya isa wurin taron jama'a, yakan zauna a ƙarshen duk inda ya iske da wuri. Ba ya tashin wani ya zauna a wurinsa. Idan mutum yana Magana da shi yakan saurare shi, ya bashi hankalinsa, sai ya gama. Ba ya yin mugun baki (watau Magana marar kyau). Ba ya la'ana. Ba ya ɗaga murya a kasuwa (Sallallahu alaihi wassallam). Ya kasance yana da kau da kai. Ba ya saka mummuna da mummuna. Kamar yadda muka faɗa a baya, ba ya yarda mutane su rufe masa baya idan yana tafiya. Ba ya nuna fifiko a kan bayinsa da masu yi masa hidima. Bai taɓa zargin wanda yake yi masa hidima ba. Yana rama hidima ga wanda ya yi masa. Wata rana yana halin tafiya tare da mutane, sai aka buƙaci  yanka akuya da gyara ta.. Sai wani daga cikinsu ya ce: "Ni zan yanka", wani ya ce,Nizan feɗe, wani ya ce: "Ni zan dafa" "Sai shi kuma ya ce:"Ni zan debo ƙirare" "Sai suka ce: "Ka bari mu za muyi". Sai ya ce: "Ba na son na fifita a tsakaninku. Allah yana ƙin bawansa idan ya ga yana fifituwa a tsakanin mutanensa". Sai ya je ya yiwo ƙiraren.

Majalisin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam), majalisi ne na nutsuwa da ladabi da aminci da girmama juna. Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana da mutuƙar nutsuwa da kwarjini a majalisin sa. Bay a yin Magana saida buƙata.. Idan yana yin Magana duk sahabbansa sukan yi tsit, su sunkuyar da kawunansu, kai ka ce tsuntsaye  ne a kawunan nasu. Ba

sa yin  musu ko jayayya a tsakaninsu. Duk wanda ya zo ya tambaye shi wata buƙata ba ya barinsa ya tafi sai ya biya masa ita, ko ya yi masa Magana mai daɗi, ta haƙurƙurtarwa.

Ya kasance ya na haɗa kan sahabbansa. Ba ya barin duk abinda zai raba tsakaninsu. Yana tambayar lafiyar duk wanda bai gani ba daga cikinsu. Idan wani ya yi abu mai kyau yana yaba masa, kamar yaddaa idan wani ya yi abu marar kyau yakan kwaɓe shi. Wani lokaci kuma yakan kawar da kansa idan ya ji wata Magana marar kyau ko wani abu marar kyau, domin su gane sun yi ba daidai ba. Yana tambayar sahabbansa halin da jama'ar gari suke ciki. Yana girmama shugaban kowace ƙabila ko dangi. Idan ya fara Magana daga ciki sahabbansa sukan dakata, sai ya gama, sannan wani ya fara tasa[6].

Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana zuwa duba marar lafiya,, ba tare da duban matsayinsa ba. Shi yake sallatar jana'iza ya bi ta har ƙabarinta. Ba ya raina gayyata ga duk wanda ya gayyace shi gidansa, ko da kuwa mace ce ko yaro.

**Halayen Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam):**

Bayan Allah ya halicci wannan Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) nasa da kyan halitta da kyan ɗabi'a sai kuma ya ɗora shi bisa kyawawan halaye. Shi da kansa Allah (Subahanahu wata'ala) ya yabe shi da cewa:

---------------------------------------------------

[6] Ar Rahikul Makhtum, sh: 417-418

"Kuma haƘiƘa kai kana kan kyawawan halaye" (Suratul Ƙalam, Aya ta:4 )

A nan za mu ga cewa duka wani kyakkyawan hali, Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya suffatu da shi. Ga kaƊan daga cikin misalansu:

**Gaskiyarsa (Sallallahu alaihi wassallam):** Gaskiyar ita ce, abinda mutum ya faɗa, ya zama haka yake a zuciyarsa, ya kuma dace da abin da yake a sarari. Haka kuma mu'amalar da mutum ya yi a bayyane ta zama haka take a zuciyarsa, matuƙar bada wani dalili na shari'ah ba.

Abin nufi a nan shi ne, Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance mai gaskiya tun a ƙuruciyarsa. Wannan ya sanya a sanda zai isar wa Ƙuraishu da aiken Allah sai da ya tara su ya ce da su: "Shin  kuna ganin idan da zan ba ku labari cewa: "Ga dawakai nan a cikin kwari, suna nufin kawo muku hari, za ku gasgata ni?. Sai suka ce: "Na'am. Ai ba mu taɓa samun ka da wani abu ba sai gaskiya". (Bukhari ne ya ruwaito).

Wani zai ce, to mene ne ƙarashen ƙissar? Ai a sannan cewa ya yi dasu: "Ni Manzo ne gare ku daga Allah, wanda idan ba ku yi imani ba azaba mai raɗaɗi za ta biyo baya". Sai suka yi shiru,

kamar za su gasgata shi. Amma ina! Baffansa Abu lahab shi ya yi wata mummunar Magana a gare shi, sannan y ace: “Yanzu domin wannan ka tara mu?. Dagan nan ya ɓata lamarin.

**Amanarsa:** Mu sani cewa, amana ba ta taƙaita ga ajjiyar dukiya kaɗai ba. Watau a bai wa mutum ajiyar dukiya ya kawo ta yadda take. Amana ta haɗa da amanar aiki (ka aiwatar da shi babu ha’inci) Amanar aiki (ka isar da shi daidai) Amanar aike (ke isar das hi daidai). Amanar Magana (ka riqe ta kada ka gaya wa wani). Ga kuma amanar gaɓɓai (kada ka aikata abin da Allah ya haramta dasu). Da sauran amanoni makamantan waɗan nan.

Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance ya shahara da amana tun kafin ya zama Manzo. Misali, tun kafin aiko shi suna yi masa laƙabi da al’aminu. Nana Khadija ta nemi ya yi mata fatauci da dukiyarta saboda labarin amanarsa da ta ji. Mutanen Makka suna bashi ajiyar dukiyarsu saboda amanarsa. Harma lokacin da zai yi hijira ya dakatar da sayyidina Ali, domin ya basu amanoninsu. Kai a taqaice dai a Tarihi cike yake ba bayanin whalar daya sha (Sallallahu alaihi wassallam), wajen isar da amanar aiken da Allah ya aiko shi da shi. `

**Cika Alqawari:** Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) Ya kasance mai cika Aqawari. Akwai misalai masu yawa game da haka. Ɗaya daga cikinsu shi ne, abin day a faru a sanda ake ƙulla sulhun Hudaibiyya. Ɗaya daga cikin yarjjejeniyar da aka rubuta akwai cewa, idan wani daga cikin kafiran Makka ya gudu Madina, a dawo da shi.. Amma idan ɗaya daga cikin musulmi masu hijira ya dawo Makka a ƙyale shi. To bayan an rubuta wannan, kafin a sa hannu, sai ga wani mutun da ake kira Abu jandal ya gudo daga hannun kafirai. Ya faɗo cikin Musulmi. Sai suhaili, (wanda yake wakiltar Ƙurashu ya ce: “Wannan shi ne wanda za’a fara mayarwa”. Sai Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya ce: “Ai ba’a gama rubutun sulhun ba”. Sai mutumin nan Ya ce: “To in haka ne ba zan yi sulhun da kai ba”. Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya yi, ya yi, mutumin nan ya ƙi yarda. Abu jandal ya dinga kuka yana cewa: “Yanzu mayar da ni za ku yi cikin kafirai, su fitini addinina! Sai Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya ce masa: “Yi haquri Abu jandal. Mun riga mun yi alƙawari da waɗan nan mutanen. Ba za mu saba ba. Allah zai ba ka mafita, kai da sauran raunana da ke tare dakai”[7]. Wannann babban misali ne na cika alqawari, wanda ba’a taɓa samun irinsa ba. Ba ma haka ba, saboda muhimmancin cika alƙawari Manzon allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya nuna baya tare da mai saɓa alƙawari, kuma ba-shi, ba-shi ranar alƙiyama.

-----------------------------------------------

[7] Bukhari ne ya ruwaito

Daga Amru binil Hamƙi y ace: “Na ji Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana cewa: “Wanda duk wani ya ba shi amincin ransa, sai kuma ya kashe shi, to ba-ni ba-shi, wanda ya yi kisan. Ko da kuwa wanda aka kasha ɗin kafiri ne” (Barrazu ne ya ruwaito a musnad ɗinsa).

**Karamcinsa (Sallallahu alaihi wassallam):** Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya zo da wani sabon launi na karamci a TArihi, wanda ba'a taɓa gani ba. Abin duniya bai taɓa rufe masa ido ba, in dai ta hanyar Allah zai bayar das hi. Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wasallam) mutum wanda ba ya tsoron talauci. Ga wani misali kaɗan na kkyautarsa a yaƙin Hunainu:

A shekara ta takwas da Hijra bayan Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya bude Makka, sai ya taho da mutum ɗari biyu sababbin musulunta, zuwa yaƙin Hunainu. Don haka rundunar Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ta zama mutum dubu goma sha biyu.

Yayin da aka kamala yaƙi, sai ya zama an sami ganima mai yawa. A nan ne fa Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya yi kyauta ta fitar hankali ga sababbin mulunta, domin ya ja hankalinsu su tabbata a wannan addini.

Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya bai wa Abu sufyanu (shugaban Makka a wannan lokacin) ruƙumi ɗari, da uƙiya arba'in na dirhami. (watau dirhami dubu da ɗari shida). Sai Abu sufyanu  ya ce: "To ga ɗana yazidu". Sai Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya bashi kwatakwacin haka. Sai ya sake cewa: "Ga kuma ɗana Mu'awiya". Sai shi ma ya ba shi kwatankwacin haka.a nan ya baiwa hakimu bin hizam raƙumi ɗari. Ya nemi ƙarin dinare dubu, ya ƙara masa.  Ya bai wa safwanu bin Umayyata dinare dubu. Ya qara masa wata dubun. Ya kuma qara masa wata dubun[8].

**Tausayisa Da Nuna Ƙauna Ga Yara:** Annnabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana da matuƙar nuna tausayi da ƙauna ga ƙananan yara. An ruwaito Hadisai kamar haka:

*Daga Nana A'isha (R.A) ta ce: "Wasu mutane sun zo wa Annabi daga larabawan ƙauye, sai suka ce: "Ku kuna*

-------------------------------------------------

Duba Ar Rahiƙul Makhtum al Mubarakafuri, Shafi na: 361. Ya curo daga littafin As daga littafin As Shufa na Alƙali Iyad.

*Sumbatar 'ya'yanku?. Sai aka ce musu "Na'am". Sai suka ce: "Mu kuwa wallahi ba ma sumbatar su". Sai Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya ce: Ban tabbatar ba ko Allah ya cire muku tausayi. Watau daga zukatanku". (Muslim ne ya ruwaito).*

*Daga 'Usamatu bin Zaid (R.A), ya ce: Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance yakan ɗauke ni ya ɗora ni a kan cinyarsa. Ya ɗora Hasan a kan ɗaya cinyar: Sannan ya rungume mu. Sannan ya ce: "Ya Allah! Ka ji tausayin su. Ni ina jin tausayin su (Bukhari ne ya ruwaito).*

*Daga Abdullahi bin Abbas (R.A) y ace: "Lokacin da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya isa Makka (a shekarar da aka buɗe Makka), sai 'yan ƙanana yara na Banu Abdul Muɗɗalib suka tare shi. Sai ya rungume ɗaya a ƙirjinsa. YA goya ɗaya a bayansa" (Bukhari ne ya ruwaito).*

**Haqurinsa Ga Masu Yi Masa Wauta:** Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya kasance mai haƙuri da kau da kai ga wanda ya nuna masa wauta ko rashin hankali. Ga wasu misalai game da haka:

*Daga Anas bin Malik (R.A) ya ce: "Na kasance ina tafiya tare da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana sanye da mayafin Najaranu mai kaurin geza, sai wani Balaraben ƙauye ya riske shi, ya fisgi mayafinsa da ƙarfi, har saida naga alamar fisgarsa daya yi a kafaɗarsa, Sai ya ce: "Ya Muhammad! Yi umarni a ba ni daga dukiyar Allah wadda take wajenka. Sai Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya waiwaya gare shi, ya yi murmushi. Sannan yayi umarni ayi masa kyauta" (Bukhari da muslim su ka ruwaito).*

Daga Ubaidullahi bin Abdullahi bin Utbatu (Ya ce,) Abu Huraira ya ba shi labari cewa, wani Balaraben ƙauye ya yi bawali a cikin masallaci (masallacin Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam)). Sai mutane suka yi kansa, za su doke shi. Sai Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya ce: "Ku ƙyale shi. Ku zuba rabin guga (ko cewa ya yi ) cikin guga na ruwa. An aiko ku masu sauƙaƙawa. Ba a aiko ku masu zafafawa ba" (Bukhari ne ya ruwaito).

**Zuhudunsa (Watau Rashin Damuwa Da Duniya):** Yadda Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya gudanar da rayuwarsa ya nuna ko kaɗan bai damu da jin daɗin duniya ba. Ya kasance yana kwanciya a kan tabarma tsirararta, da matashi wanda aka cusa masa zarbar dabino. Galibin abincinsa dabino da sha'ir. Akwai lokutan da akan shafe wata biyu ba a yi girki ba a gidansa, sai dabino da ruwa. Wasu maƙotansa ne masu kiwo sukan aiko musu da nonon awaki. Ga dai wasu Hadisai da suke nuna irin rayuwar da ya yi (Sallallahu alaihi wassallam).

*Daga Nana A'isha tace: "Iyalin Annabi Muhammad basu taɓa ƙoshi da abincin alkama ba dare uku a jere, tun daga sanda ya isa Madina" (Bukhari da muslim ne suka ruwaito)*

*Daga Nana A'isha Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya rasu, alhali bai taɓa ƙoshi da gurasa da mai ba sau biyu, a rana ɗaya" (Muslim ne ya ruwaito).*

*Daga Anas bin Malik (R.A), ya ce: "Annabin Allah (Sallallahu alaihi wassallam) bai taɓa cin abinci a kan tebur ba ko a cikin faranti ko gurasa da romo".[10]*

*Daga Abu Huraira (R.A) ya ce: "Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya ce: IDan da a ce, ina da zinare kwatankwacin dutsen uhudu, ba zan ji daɗi ba a ce na yi kwana uku da ragowarsa a tare da ni. Sai a bin da zan ajiye domin na biya bashi" (Bukhari ne ya ruwaito).*

---------------------------------------------

Amma fa wannan baya  nufin yin haka haramun ne ko makaruhi. Yana cikin babin Zuhudu. Watau rashin damuwa da kyale duniya

**Jarumtarsa (Sallallahu alaihi wassallam):** Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) jarimi ne, wanda ba'a taɓa ganin irinsa ba. Ga dai abinda wasu daga cikin sahabbansa suke cewa:

*Barra'u bin Azib (R.A) ya ce: "Wallahi duk sanda yaƙi ya runcaɓe, da shi muke yin kariya. Jarumi daga cikinmmu shi ne wanda yake jeruwa da shi (Muslim ne ya ruwaito).*

*Daga Anas (RA) ya ce: Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya ksance ya fi kowa kyau. Ya fi kowa kyauta. Ya fi kowa jarumta. Wata rana mutanen Madina sun ji wata ƙara cikin dare. Sai mutane suka nufi wajen ƙarar. Sai Annabi ya tare su, alhali ya riga su zuwa wajen ƙarar, yana cewa: "Kada ku damu, kada ku damu". Yana kan wani doki na Abu Ɗalha ko sirdi babu. Yana rataye da takobi…" (Bukhari da muslim suka ruwaito).*

**KASHI NA UKU**

**Koyi Da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam)**

**Wajibcin koyin da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam):**

Ita masa'alar koyi abu ne wanda yake haɗe da halittar ɗan adam. A farkon rayuwar dan'adam yakan fara koyi da duk abin da ya ga ana yi, ko daga wajen wa ya ga abin. Yayin da ya buxe ido ya gane iyayensa, to sai kuma ya koma koyi dasu. To shi kansa wannan matakin akwai matsalarsa, idan ya zama su iyayen ba a kan shiriya suke ba. Shi ya sa alƙur'ani ya yi ta fama da masu maƙalƙale wa iyayensu wajen koyi dasu a mummunar hanya. Misali, inda Allah (Subahanahu wata ala) yake cewa:

"*Idan aka ce dasu: "Ku bi abinn da Allah ya saukar. Sai suce "A'a, mu kawai za mu bi abin da muka saba iyayenmu suke kai ne. (Allah Subahana wata ala yace: "Yanzu sa sa riqa bin iyayen nasu) Ko da iyayen nasu bas u da hankalin fahimtar abubuwa, kuma basa kan shiriya?" (Suratul Baƙarah, aya ta:170).*

Wani lokaci kuma mutum yakan ga wani wanda ya burge shi a wata kwarewa ta rayuwa, misali: kwararren mai tunani wanda ya ƙirƙiri wata hanya ta rayuwa. (kamar kwamanisanci, ko jari hujja. Ko wanda ya ƙirƙiro wani tsari na shugabanci. (kamar damakwaraɗiyya) ko ƙwararren ɗan siyasa wanda ya yi shuhura. Ko ma ƙwararren ɗan wasa ko ƙwararren jarimi a wani fim ko

wasannin  kwaikwayo. Idan ba’a yi sa’a ba sai mutum ya kama ɗaya daga cikin waɗan nan ya zam abin koyinsa a rayuwa. Ka ga an shiga cikin vata marar iyaka.

Wannan ya sa Allah (Subahanahu wata ala) ya yi ta aiko da manzanni domin a yi koyi dasu, Allah (Subahanahu wata ala) yana cewa:

“Waɗan nan su ne waɗanda Allah ya shiryar. Ka yi koyi da shiriyarsu” (Suratul An’am aya ta:90).

To kasancewar Annabinmu (Subahanahu wata ala), shine na ƙarshe a cikin manzannin Allah, sai ya  zama shi Allah ya sanya mana ya zama abin koyinmu. Allah (Subahanahu wata ala) yana cewa:

“HAƙiqa  kyakkyawan koyi ya tabbata a gare ku, daga Manzon Allah, ga wanda yake ƙaunar Allah da (kyakkyawar makoma daga) Allah da ranar lahira, kuma,  ya ambaci Allah da yawa” (Suratul ahzabi, aya ta:21).

Wannan ya nuna wajibcin anya shi abin koyi a dukkanin hanyoyin rayuwa.

**Koyi da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) a dukkanin tsare-tsaren rayuwa:**

Duk Wanda yace shi Musulmi ne, to lallai ne abin koyinsa ya zamo Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam), a dukkanin tsare-tsare na rayuwarsa. Misali: Tsarin Ilimi, tsarin zamantakewa, tsarin Tattalin arziƙi, tsarin siyasa (shugabanci) da tsarin shari’ah. Abin nufi a nan shi ne, duk waɗan nan tsare-tsare na rayuwa su zamo a kan tsarin alqurani da sunnah, bisa fahimtar magabata na ƙwarai. Kada mutum ya zama sai a sallah, Azumi, aikin Haji kaɗai, yake Musulmi. Watau ya zama yana bin tsarin da ya saɓa wa na Allah. Allah (Subahanahu wata ala) Yana cewa:

“Ya ku waɗanda suka yi imani! Ku shiga Musulunci gaba ɗaya (watau ku miƙa wuya gaba ɗaya). Kada ku bi takun sheɗan, ba na Allah ba). Shi abokin gaba ne a gare ku, bayyananne” (suratul BAƙarah, Aya ta: 208).

Abin takaici shi ne, a halin da muke ciki a yanzu, za mu ga cewa a dukkanin tsare-tsare nan na rayuwa babu wanda muke tafiyar da shii a kan tsarin da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) ya zo da shi. Misali: Tsarin Iliminmu baya  koya mana tauhid da tsoron Allah da ranar lahira da Tarbiyyar Musulunci. A tsarin zamantakewa. Idan muka ɗauki zamantakewarmu ta aure da zaman iyali, ba akan alƙur’ani da sunnah take ba. Tsarin Tattalin arzikinmu cike yake da cin hanci da rashawa, cin Riba, gululu’ (Watau satar dukiyar jama’a) da sauransu. Tsarin siyasarmu (shugabanci) tsari ne na Damakwaraɗiiyya, wanda babu Allah a  cikinsa. Shi kuwa tsarinmu na shari’ah kowa ya san dokokin ‘yan’adam muke fifitawa a kan dokokin Allah (Subahanahu wata ala). Abin nufi a nan shi ne, son Annabinmu  na baka ne kawai. Ba a aikace yake ba. Gashhi kuwa Allah (Subahanahu wata ala) yana cewa:

*“Gaya musu, idan ku kasance kuna son Allah, to ku bi ni, sai Allah ya so ku, ya gafarta muku zunubanku. Allah mai gafara ne, mai rahama” (Suratu Ali Imrana, Aya ta:31)*

Allah (Subahanahu wata ala) yana cewa: “Ka ce musu Idan iyayenku da ‘ya’yanku da ‘yan’uwanku, da matanku, da danginku da dukiyoyinku da kuka nema da hanyar samunku da kuke gudun kada ta yi tasgaro da gidajen da kuke jin daɗinsu, su suka fi soyuwa a gare ku, maimakon Allah da Manzonsa, da ƙoƙarin tabbatar da tsarinsa, to ku zauna, har sai Allah ya zo da lamarinsa (Mutuwa ko halakarwa). Allah ba ya shiryar da mutane fasiƙai” (suratul Taubah, Aya ta:24).

Wannan duka yana nuna cewa ba za mu zama Musulmi ba sai mun gudanar da kowane ɓangare na rayuwarmu bisa tsarin Allah. Wannan kuma ba zai samu ba sai ta hanyar koyi da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam), watau ta hanyar ruƙo da alƙur’ani da Sunnah. Annabi(S.A.W) ya ce:

*“Na bar muku nauyaya guda biyu, ba za ku ɓata ba, matuƙar kun yi ruƙo da su: Littafin Allah da sunna ta”*

**Yadda Sahabbai Suka Yi Koyi Da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam):**

Sahabban Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassal) sun yi koyi da shi a cikin dukkanin harkokin rayuwarsu. Ba kawai sai a salla, Zakka, Azumi da Hajji kaɗai ba. Ga wasu misalai ‘yan kaɗan da za su nuna mana haka.

Dab da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) zai yi wafati ya zartar da wata rundina ta yaƙi, qarqashin shugabancin Usamatu bin Zaid. Bayan wafatin annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) sai wasu suke ganin ya kamata a dakatar da wannan runduna tukuna, kasancewar an sami wasu suna ƙin bayar da zakka. Har ma aka zama cikin tsoron kawo hari cikin Madina. Me Abubakar yayi a matsayinsa na shugaba? Abubakar bai yarda a dakatar da wannan runduna ba. Cewa ya yi:

“Ba za ta yiwu ba a gare ni na kwance tutar da Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya qulla”.

Haka nan sauran sahabbai suka goyi bayan Abubakar, Usamatu ya shugabanci wannan yaƙi kuma aka yi gagarumar nasara. Game da Madina kuwa, abin da Abubakar yayi shi ne, sai ya sanya wasu daga cikin manyan sahabbai suka shugabanci wata runduna domin bat a kariya, kamar su: Aliyyu bin Abi Ɗalib, zubairu binil Auwam, sa’adu bin Abi Waƙƙas, Abdullahi bin Mas’ud da abdur Rahman bin Aufin[12].

Wani abin da sayyidina Abubakar ya yi (na ruƙo da tsarin Annabi) bayan wafatinsa (Sallallahu alaihi wassallam), wanda yake nuna dagewarsa, shi da sauran sahabbai, a kan

---

[12] https://www.mominoun.com/articles

Sunnar Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) (watau tsarin sa na rayuwa) shi ne, wasu Larabawan ƙauye sun ƙi bayar da zakka bayan wafatin AnnabiMuhammad(Sallallahualaihiwassallam). A wannan lokacin cewa ya yi:

“Wallahi! Idan da za su hana ni dabaibayi, wanda suka kawo wa Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam), da sai na yaƙe su”.

Wani abin da za mu sake lura das hi shi ne, yanayin da Nana faɗinmah ‘yar Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ta nemi gadon Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam), a nan ma sai ya ce mata ya ji Manzon Allah ya ce:

“Mu jama’ar Annabawa ba a gadon mu. Abinda muka bari, sadaka ne” (Bukhari da muslim ne suka ruwaito).

Wani misali shi ne, wata rana sayyidina Umar ya zo zai sumbaci Hajarul Aswadi sai ya tsaya ya ce:

“Ni na san kai dutse ne. Ba ka cutarwa, ba ka amfanarwa. In ba domin na ga Annabi (Subahanahu wata ala) ya sumbacce ka ba, da ba zan sumbace ka ba”. (Bukhari ne ya ruwaito).

Wata rana Abdullahi bin mas’ud ya zo zai shiga masallaci sai ya ji Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam) yana cewa: “A zauna”. Sai ya zauna a kan dokin ƙofar masallaci. Bai ƙara yin gaba ba ko kaɗan, sabo da cika umarni.

Haka nan sahabbai suka yi ta koyi da Annabi Muhammad (Sallallahu alaihi wassallam), a dukanin tsare-tsaren rayuwa. Wata rana Abdullahi bin Mugaffal ya ga wani mutum (ko wani ɗan ɗan uwansa), yana yin jifan da ake kira ‘Hazfu (wadda akan sa tsakuwa atsakanin babban danyatsa da ɗab ali, awulla ta). Sai ya ce da shi: “Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya hana yin hazfu. Daya sake ganinsa yana yi sai ya ce: “Ina gaya maka Manzon Allah (Sallallahu alaihi wassallam) ya hana yin hazfu kana sake yi. Ba zan sake yin Magana da kai ba, har abada” (Bukhari da Muslim ne suka ruwaito).

Har ma ta kai cewa wasu daga cikin sahabbai suna koyi da Annabi, hatta a abubuwan da Annabi yakan yi ba da nufin lallai sai an yi koyi da shi ba.

Abdullahi bin Umar ya shahara game da haka.

Abdullahi bin Umar ya kasance yana zuwa ƙarƙashin wata bishiya a Madina, ya yi baccin rana. Da aka tambaye shi game da haka, sai ya ce shi kawai ya ga Annabi yana yin baccin rana a ƙarƙashinta.

Wata rana Abdullahi bin Umar yana cikin tafiya tare da mutane, sai aka ga ya kewaye wani wuri, bai bi ta wurin ba, (Alhali ba bu komai a wurin), da aka tambaye, shi sai ya ce ya ga Annabi wata rana suna tafiya ya kewaye wurin.

Haka nan wata rana an ga ya sauka a wani wuri tsakanin Makka da Madina, ya yi salla a diadai wannan wurin suna halin tafiya. Duk da kasancewar a lokacin mutane sunyi masallaci a kusa da wurin shi sai ya ƙi yin salla a masallacin, ya je ya yi a daidai inda Annabi ya yi (Sallallahu alaihi wassallam).

## KAMMALAWA

Godiya ta tabbata ga Allah (SWT), wanda ya shiryar da ni, ya ba ni ikon kamala rubutun wannan littafi a yau Litinin 8 ga Watan Zul Ƙidah 1441, wanda ya yi daidai da 29 ga watan Mayu 2020.

Ina roƙon Allah (SWT) ya sa wannan ɗan littafi ya zamo mai amfani ga Musulmi. Ya zamo ta hanyarsa mun san kamannin wannan shugaba namu da suffer halittarsa. Mu san kyawawan halayensa. Manufa a ƙarshe it ace, mu yi koyi da shi a dukkanin harkoki da tsare-tsare na rayuwarmu. Allah ya sa haka, amin.

Dr. Yahaya Tanko